

HA

# “Na nemi makafa a EU – wace kasa ce za ta kula da bukatata?”

A

Bayanai game da Dukar Dublin don neman damar kariyar kasa da kasa dangane da sashe na 4 na dokar (EU) mai lamba 604/2013

Ka bukaci mu baka ka kariya saboda ka kula da cewa an tilasta maka barin kasarka saboda domin hukumtarwa, yaki ko hadarin cutarwa mai tsanani. Doka na kiran wannan ‘neman damar/bukatar kariyar kasa da kasa’ kuma kai – ‘mai neman dama’. Ana kiran mutane masu neman kariya a matsayin ‘masu neman kariya’

**Domin kana bukatar makafa a nan ba zai tabbatar da cewa za mu bincika da bukatarka a nan. Ana zabar kasar da za ta bincika bukatarka ne ta hanyar wani tsarin wanda dokar Tarayyar Turai ta kirkira wanda aka sani da Dokar ‘Ddubin’. Kamar yarda wannan doka ta nuna, kasa daya kacal ce ke da hakkin bincika bukatarka.**

Wannan dokar tana aiki a duka wani yankin da ya kumshi kasashe 32. Muna kiran wadannan kasashe 32 da suna ‘kasashen Dublin’ a wannan takardar takaitaccen bayani.

**Idan akwai wani abu a cikin wannan takardar takaitaccen bayani da baka fahinta ba, ka tambayi hukumominmu.**

Kafin a kula da bukatarka ta neman makafa, muna bukatar mu tabbatar da cewa mune muke da hakkin bincika ta ko kuma kila wata kasa ce ke da hakkin – muna kiran wanna da suna ‘tsarin Dublin’. Tsarin Dublin ba zai shafi dalilinka na neman makafa ba. Zai kula ne kawai da tambaya akan wace kasa ce ke da hakkin shawara akan takardarka ta neman damar makafa.

**Wannan takardar takaitaccen bayanai tana ba da bayani ne kawai. Burinta shine samar da muhimman bayanai ga masu neman kariyar kasa da kasa a kan abinda ya shafi Tsarin Dublin. Ba ta kirkira/kumshi dama ba da kanta ko doka Dokoki da hakkin na Kasashe da mutane a karkashin tsarin Dublin sunanan kamar yarda suke a Dokar (EU) 604/2013.**

**©European Union 2014**
**An amince sake bugawa. Dole ne a nema samin dama daga masu ikon bayar da dama domin anfani ko sake buga hoton wani mutum**




*Wadannan kasashen Dublin sun hada kasashe 28 na Hadin kan Turai (Austria (AT), Belgium (BE), Bulgaria (BG), Croatia (HR), Cyprus (CY), Czech Republic (CZ), Denmark (DK), Estonia (ET), Finland (FI), France (FR), Germany (DE), Greece (EL), Hungary (HU), Ireland (IE), Italy (IT), Latvia (LV), Lithuania (LT), Luxembourg (LU), Malta (MT), Netherlands (NL), Poland (PL), Portugal (PT), Romania (RO), Slovakia (SK), Slovenia (SI), Spain (ES), Sweden (SE), United Kingdom (UK)) har da kasashe hudu “masu alaka” da Dokar Dublin (Norway (NO), Iceland (IS), Switzerland (CH) da Liechtenstein (LI)).*

## “Wane tsawonlokaci za dauka domin shawarta wace kasa ce za ta kula da takardar neman damata? “

## “Wane tsawon lokaci zai kasance kafin a bincika takardar neman damata?”

Idan hukumominmu suka shawarta cewa mu ne muke da hakkin shawara akan takardarka ta neman damar samin makafa, wannan na nufin cewa za ka saura a wannan kasa kuma a bincika takardar neman damarka anan. Za a fara shirin bincika takardar neman damarka nan take.

Idan muka yi shawara cewa wata kasa ce ke da hakkin akan takardar neman damarka, za mu bakaci aika ka zuwa waccar kasar ba tare da bata lokaci ba domin a kula da takardar neman damarka a can. Gabadaya lokacin tsarin Dublin, har zuwa lokacin da za a mayar da kai zuwa waccar kasar **zai, a cikin komi yana daidai, yana daukar tsawon watanni 11**. Sannan za a bincika bukatarka ta neman makafa a kasar da ke da hakkin. Wannan lokacin na iya banbanta idan ka boye daga hukumomin, ka shiga kaso ko kulle, ko idan ka daukaka karar shawarar mayar da kai. Idan kana daya daga cikin wadannan halaye, za ka sami bayanai na musamman, da suke baka bayani akan tsawon lokacin da shafeka. Idan an kulle ka, za a sanr da kai dalilin kullewar da kuma mafita ta hanyar sharia da kake da su.



©European Union

## “Ta yaya aka shawarta kasar da ke da hakkin takardar neman damata”



©iStockphoto / Joe Gough

Dokar ta fitar da dalilan da yasa wata kasa za ta kasance da hakkin bincika bukatarka. Ana kulawa da wadannan dalilai ta hanyar muhimmanci a doka, farawa daga idan kana da dan’uwa a waccar kasar Dublin; idan taba samin visa a yanzu ko a da ko takrdar zaman kasa wanda wata kasar Dublin ta baka; ko kuma idan ka taba balaguro zuwa, ko ta cikin, wata kasar Dublin, ko ta hanyar doka ko ba sosai ba.

**Yana da muhinmanci ka sanar da mu tunda wuri idan kana da yan’uwa wata kasar Dublin**. Idan mijnki, matarka ko danka/yarka ya kasance mai neman damar samin makafa ko an bashi kariyar kasa da kasa a wata kasar Dublin, waccar kasar za ta kasance mai hakkin binciki takardarka ta neman damar samin makafa.

Za mu iya shawarar bincika takardar neman izininka a wannan kasar, koda ya kasance wannan bincike ba hakkinmu bane a tsarin dokar Dublin. Ba za mu aika ka zuwa kasar da aka sani cewa za a iya cin zarafin hakkinka.



## “Menene zai faru idan bana son zuwa wata kasar?”

Kana da yiuwar kace ka ba ka aminta da shawarar aika ka zuwa wata kasar Dublin ba, kuma ka iya kai karar wannan shawara a gaban kotu ko majalisar masu sharia. Kana kuma iya bukatar kasancewa a wannan kasa har sai an shawarta akan daukaka kararka ko sake dubawa.

Idan ka yi watsi da takardar neman damar samin makafarka kuma ka tafi zuwa wata kasar Dublin, za a iya dawo da kai zuwa wannan kasar ko kasar da ke da hakki akan ka.

**Yana da muhimmanci ka kasance a wannan kasa, da zarar ka nemi damar samin makafa har sai mun yanke shawara akan kasar da ke da hakkin bincika bukatar neman makafarka kuma/ ko a bincika bukatar neman makafarka a wannan kasar.**

**Ka sani cewa idan muka kula cewa za ka iya guduwa or boye mana saboda ba ka so mu aika ka zuwa wata kasa za a iya kulle ka (wata cibiya ta kusa). Idan hakane, kana da damar daukar wakilin shari’a kuma za mu sanar da kai game da suaran dama da kake da ita, tare da damar daukaka kara akan kulle ka.**



©iStockphoto / janp013

## “Menene yasa ake bukatar daukar zanen yatsuna?”

Idan ka shigar da bukatar neman samin makafa, ida kana dan shekaru 14 ko sama da kaka, za a dauka zanen yatsunka kuma a tura zuwa ma’adanar zanen yatsu mai suna ‘Eurodac’. **Dole ne ka hada kai da wannan tsari – doka ta tilasta maka daukar hoton zanen yatsunka.**

Idan zanen yatsunka basu da kayua, tare da idan ka bata yatsunka da gangan, za a dauka hoton zanen yatsun a gaba.

Za a bincika zanen yatsunka a tsakani Eurodac to domin gani ko ka taba neman damar samin makafa a da ko domin gani ko an taba daukar hoton yatsunka a wata boda. Wannan yana taimakawa wajen gano ko wace kasa ce ke da hakkin bincika da bukatar samin makafarka.

Za kuma a iya bincika zanen yatsunka ta hanyar Jerin Bayanan Bisa (VIS) wanda ya kasance wata ma’adanar bayanai da ke kumshe da bayanai da ke dangance da visa da aka bayar a tsakanin kasashen Schengen. Idan kana da sabo ko tsohon bisa na wata kasar Dublin, za a iya aika ka can domin kula da bukatarka ta neman kariyar kasa da kasa.

Yayin da ka nema damar samin makafa, Eurodac ne zai adana bayanan zanen yatsunka har tsawon shekaru 10 – bayan shekaru 10, za a share da Eurodac ta otomatik. Idan ka yi dace da bukatarka ta neman makafa, zanen yatsunka zai kasance a ma’adanar bayanai har sai an share su ta otomatik. Idan ka zama dan kasar Dublin, za a share zanen yatsun nan take. Za a adana zanen yatsunka da jinsinka a cikin Eurodac – ba za a aika da sunanka, hotoka, ranar haihuwanka zuwa ma’adanar Eurodac ba, amma za a iya adana su a ma’adanar bayanai ta kasa.

Kana iya tambayarmu a gaba game da bayanan da suka shafe ka da muka nada a Eurodac. Idan kana ganin cewa bayanan suna da kuskure ko kuma bai kamata a adana su ba, kana iya butakar a gyara ko share su **Za a iya samin bayanai game da hukumomin da ke da hakkin kula da (ko Kula) bayananka a wannan kasa da kuma hukumomin da ke hakkin lura da kariyar bayanai a shafi na 11.**

Wata Hukumar Hadinkan Turai mai suna eu-Lisa ce ke gudanar da Eurodac. Za a iya anfani da bayaninka ne akan abin da ya shafi doka kawai ne. Cibiya Eurodac ce kawai za ta iya karbar bayananka. Idan ka bukaci neman makfa a wata kasar Dublin a nan gaba, za a aika da zanen yatsunka zuwa waccar kasa domin tabbatarwa. Ba za a raba bayanan da aka adana a Eurodac tare da wata kasa ko kugiya da ba ta kasashen Dublin ba.

Hukumomi kamr yansanda da kuma ofishin yansandan Turai (Europol) za su iya bincika zanen yatsun a ranar 20 July 2015 inda za su iya bukatar iso ga ma’danar bayanai ta Eurodac domin kariya, sharewa da kuma binciken iyagun aiyuka da ta’addanci.

## “Mecece damata yayin da kasar da ke da hakkin take shawara akan bukatata ta neman makafa?”

Kana da damar kasancewa a wannan kasa idan mu ne ke da hakkin kula da bukatar neman makafarka, ko, wata kasa ce ke da hakin, har sai an mayar da kai can. Idan wannan kasar ce ke da hakkin bincika bukatar neman makafarka, kana da damar kasancewa a nan har sai an yanke shawarar farko game da takardar neman damar makafarka. Kana kuma da damar cin anfanin yanayin karbar kayayyaki, kamar mahalli, abinci da sauransu, har ma da kula da lafiya da kuma taimakon kula da lafiya na gaggawa. Za a baka damar bamu bayanai game da halin da kake ciki da kuma kasancewar yan'uwanka a kasar Dublin a bayyane/ko a rubuce kuma, yayin yin haka, kana iya yin anfani da harshenka na asali ko wani harshe da fahimta sosai (ko ka sama mai fassara, idan kana bukata) Za kuma ka karba kwafi na hukumcin mayar da kai zuwa wata kasa. Kana kuma da damar da za ka tuntube mu domin karin bayani da/ko ka tuntuba ofishin Komishinan Kana kuma da damar da za ka tuntube mu domin karin bayani da/ko ka tuntuba ofishin Komishinan Yan gudun Hijira na Majalisar Dinkin Duniya (UNHCR) a wannan kasar.

**Idan muka kula cewa wata kasa ke da hakkin bincika takardar neman damarka, za ka sama cikakken bayani game da waccan shiri da kuma yadda zai shafeka dadamarka.**




## Bayanan abokin ma'amala:

**Cikakkun bayanan abokan ma'amala na hukuma samin makafa**
Maahanmuuttovirasto (Hukumar Kula da Shige da Ficen Finish)
PL 10, 00086
Maahanmuuttovirasto
+ 358 295 419 600
www.migri.fi

**Cikakkun Bayanan Abokan Ma'amala na Hukumar Lura ta Kasa the (Kariyar Bayanai)**
Tietosuojavaltuutetun toimisto (Ofishin Kariyar Bayanai)
PL 800, 00521 Helsinki
+ 358 295 666 700
Jagoran tarho:
+358 295 666 777
Litinin-Jumma'a karfe 9-11
tietosuoja@om.fi
www.tietosuoja.fi

**Gano mai kula da Eurodac da wakili/wakiliyarsa**
Mazauni abokan ma'amala:
Rundunar Yan Sandan ta Kasa (Poliisihallitus) da Hukumar Kula da Shige da Ficen Finish (Maahanmuuttovirasto)

**Cikakkun bayanai na ofishin mai kula**
+ 358 295 480 181
Poliisihallitus (Rundunar Yan Sandan ta Kasa)
PL 22, 00521 Helsinki
kirjaamo.poliisihallitus@poliisi.fi

Maahanmuuttovirasto (Hukumar Kula da Shige da Ficen Finish)
PL 10, 00086
Maahanmuuttovirasto
+358 295 419 600
www.migri.fi

Idan kana so ka duba bayani da ya shafe ka wanda aka nada a sistem din Eurodac, bayar da wata bukat ofishin yansanda. Ka shiya da nuna wasu shaidu na kanka. Muna ba da shawara ka tuntuba ofishin yan sandan da ya karba takardar neman damar samin makafarka. Akwai bayanan abokan ma'amala na ofishin yansandan a Sashen Yanar Gizo na Yansanda a poliisi.fi.

**Ofishin masu ba da taimakon shari'a da Kungiyoyin goyon bayan yan gudun hijira**
Ana samun taimakon shari'a daga ofishoshin sharia da kuma atoni wadanda suka sanar cibiyar

karbar baki game da shirinsu na taimakawa mai neman makafa. Domin karin bayani game da taimakon shari'a, yi magana da ma'aikatan cibiyar karbar baki.

**Cikakkun bayanan tuntubar Ofishi na Kasa na Kungiyar 'Yan Gudun Hijira ta Duniya (IOM) a Finland**
IOM Finland
Unioninkatu 13, bene na 6
PL 851, 00101 Helsinki
+358 9 684 1150
fiavrrcases@iom.int
www.iom.fi

Idan kana so ka koma kasarka ta asali da kanka, nema shawara a cibiyar karbar baki.

**Ofishin Babban Komishinan Yangudun hijira na Majalisar Dinkin Duniya mafi kusa**
UNHCR
Sveavägen 166, 15th floor
SE-11346 Stockholm
SWEDEN
tel. +46 10 10 12 800
swest@unhcr.org

European Commission
Maahanmuuttovirasto
Migrationsverket
Finnish Immigration Service
POLIISI
POLISEN I FINLAND
Police of Finland
Rajavartiolaitos
Gränsbevakningsväsendet
The Finnish Border Guard

1.8.2019 - hausa